# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Aljannar Kare – Haɗarin afkawa cikin bashi
## Kashi na bakwai: Haɗarin fuskantar shari'a


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | James Muhando |
| Wanda ya fassara: | Danlami Bala Gwammaja |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Mai ba da labari: | ɗan shekara 30 |
| Ado: | ɗan shekara 45 |
| Sabis: | ɗan shekara 30 |
| Kwastoma a mashaya: | ɗan shekara 30 |
| Yallaɓai: | ɗan shekara 50 |
| Jamila: | 'yar shekara 15 |
| Bash: | ɗan shekara 15 |
| Kawu Natanko: | ɗan shekara 45 |
| Mai shari'a Magajiya: | 'yar shekara 40 |
| Mai gabatar da ƙara: | ɗan shekara 40 |
| Ali: | ɗan shekara 15 |
| Sakatariya: | 'yar shekara 25 |
| Nana: | 'yar shekara 35 |
| Lawan: | ɗan shekara 35 |

**Mai ba da labari:**

Jama’a ina yi muku barka da zuwa ofishina da kuma shirin “Ji Ka Karu”. Idan ba ku manta ba, ni ne abokin hirarku a cikin shirin nan mai suna “Aljannar kare – Haɗarin afkawa cikin bashi”. Sunana dai… Don Allah ku yi mini haƙuri kaɗan. … E, Aliyu Bello ne, jami’i mai kula da harkokin ba da bashi na Bankin Simba ba. … Me kake buƙata? … To riƙe waya, bari na haɗa ku. To, bari mu bar maganar waya haka nan, mu yi batun rayuwata ta da, da kuma yadda bashi ya jefa mu, ni da abokaina, cikin matsaloli masu yawa.

A wancan kashin, na faɗa muku yadda iyayena suka gano na ɗauki rikodar Kawu Natanko na bayar da ita a matsayin kadarar bashin da abokina Bash ya karɓa. Daga nan kuma wasu ’yan daba suka kai wa gidanmu farmaki a yayin da suke neman kawun nan nawa, iya-rigima, wanda ashe shi da ma ya sha ta fi ƙarfin cikinsa. Jami’in ’yan sandan ƙauyenmu shi ne ya kama waɗannan ’yan daba. Ya kuma yi mana alƙawarin nemo Malam Ado mai bayar da bashin nan da ya karya wa Jamila hannu a garin neman mu biya shi kuɗinsa. Sun kuwa samo waɗannan marasa gasikiyar a wata matattarar irinsu, wato mashaya a ƙauyen Kwazaye.

**Fitowa ta 1: An kama Malam Ado a mashayar Kwazaye**

| | |
|---|---|
| **Ado:** | Kai Sabis! Ka kawo mini giya! |
| **Sabis:** | To, ina zuwa! … Mutumina, nawa ma ka ba ni? |
| **Kwastoma:** | Dala biyu na ba ka. Ga kuɗin nan a hannunka fa! |
| **Sabis:** | Uhmm! Ina ruwan sarkin shirme! Ban san me ya same ni ba yau. Duk na bi na ruɗe! |
| **Ado:** | Kai, ka kawo min giya na ce! Me yake damunka? Ko ka ɗauka ba ni da kuɗi ne? |

**Sabis:** Ina zuwa fa na ce! Ba fa kai kaɗai ba ne ba fa!

**Yallaɓai:** Shi ne wancan?

**Jamila:** E, shi ne.

**Bash:** Wancan shi ne, Yallaɓai!

**Yallaɓai:** Malam Ado, an kama ka saboda damfarar waɗannan yaran da ka yi, ka kuma yi sanadin karyewar hannun Jamila! Kada ma ka fara tunanin guduwa don kuwa duk inda ka je, sai na kama ka.

**Ado:** Ba wanda ya isa ya kama Ado! Ba za ka iya tsorata ni ba!

**Yallaɓai:** Kai! Kawo hannunka nan!

**Ado:** Ka rabu da ni! Ka rabu da ni na ce! Ni ba ɓarawo ba ne!

**Yallaɓai:** Zo mu tafi!

**Mai ba da labari:**

Wannan shi ne farkon tabbatar da adalci. Bayan kwana biyu kuma sai aka kama Kawu Natanko a wani gari kusa da namu. Wani tsohon abokin kawun nawa ne mai suma Malam Audu Sani ya kai ƙararsa wajen 'yan sanda saboda wata damfarar da ya yi masa! In da a lokacin na kai matsayin mai kula da harkokin ba da bashi, to da zan shawarci Kawu Natanko da ya rage kashe kuɗi ya dinga yin tari! Don komai ƙanƙantar abin da kake ajiyewa zai yi ma'ana! Sannan kuma za ka duba yiwuwar buɗe hanyoyin samunka. To wallahi, gara a ce ka yi haka da ka yi ƙoƙarin Kawu Natanko.

**Fitowa ta 2: A kotu, an ɗaure Kawu Natanko**

**Mai shari'a Magajiya:** Kowa ya yi shiru! … Mai gabatar da ƙara.

**Mai gabatar da ƙara:** Na'am, ranki ya daɗe!

**Mai shari'a Magajiya:** Kammala jawabinka!

**Mai gabatar da ƙara:** Ranki ya daɗe, kamar yadda kika sani, ɗabi'ar wasu daga mutanenmu ne su ci bashi, amma ba su da niyyar biya. Waɗansu mutanen kuma, kamar dai wanda ake tuhumar nan, har damfarar mutane suke yi, su damfari bankuna, wani lokacin ma har su yi sata, saboda a ko da yaushe ba su da aiki sai shan giya da caca, kuma duk waɗannan dabi'un za a iya kauce musu! Saboda haka, ina roƙon wannan kotu ta yi wa wanda ake tuhumar nan hukunci mai tsanani! Don abin ya zama darasi a gare shi nan gaba da ma duk wani mai hali irin nasa. Na gode, ranki ya daɗe!

**Mai shari'a Magajiya:** Kowa ya yi shiru! A yi mana shiru! Kai Natanko Bello, kana da ta cewa?

**Kawu Natanko:** Ranki ya daɗe, na riga na faɗi duk abin da zan ce yayin da na yi jawabina.

**Mai shari'a Magajiya:** To shi ke nan. A kundin shari'a ta tsarin zamantakewa, a ƙarƙashin sashe mai lamba 595, sakin layi na 7, wannan kotu ta sami wanda aka yi ƙara, Natanko Bello, da laifin karɓar Dala 400 ta hanyar zamba cikin aminci daga wajen Malam Audu Sani, da kuma damfarar bankuna masu yawa kuɗaɗe waɗanda ya ranta kuma ya ƙi biya. A saboda haka na ɗaure shi shekara biyu.

**Kawu Natanko:** Wayyo Allahna! Na shiga uku! Shekara biyu!

**Mai shari'a Magajiya:** A yi shiru! Kowa ya yi shiru! Na kuma bayar da umarnin cewa, mai laifin, yayin da yake zaman jarun, ya dinga halartar darasi na sati-sati inda zai koyi yadda zai rage halayensa na caca da shan giya da kuma cin bashi barkatai. Magatakarda, ka tabbatar an zartar da wannan umarnin! Kotu ta tashi.

**Mai ba da labari:**
To amma fa mu ma ba mu sha ba, don kuwa sai da jami'in 'yan sandan nan ya sa aka yanke mana hukuncin tsaftace caji'ofis ta hanyar nome ciyawa na sati guda. Sannan mu ma kamar Kawu Natanko, sai da aka umarce mu mu dinga halartar darasi a kan cin bashi.

**Fitowa ta 3: A caji'ofis**

**Jamila:** Duk wannan ya same mu ne saboda wani cin bashi na banza!

**Bash:** Mitar me kike yi ne? Babu fa abin da kike yi ban da tsince takardu, mu kuma ga shi fama muke ta yi da adduna!

**Jamila:** Ka faɗi haka mana, tun da ba kai ne da karyayyen hannu a rataye ba! Duk wannan kai ne ka jawo mana!

**Bash:** Haba Jamila! Ba na wurin lokacin da hannunki ya karye!

**Jamila:** Amma ai kai ka jawo mana. Ba don ka je ka saci sahannun babanka ka karɓi bashin keke ba, ai da duk wannan ba ta faru ba!

**Ali:** To ko ma mene ne dai, ai ya riga ya faru! Maimakon mu tsaya muna zargin juna, me zai hana mu dinga yi wa junanmu nasiha!

**Jamila:** A kan me?

**Ali:** A kan yadda za mu rayu ba tare da cin bashi ba mana.

**Bash:** To sarkin hangen nesa, faɗa mana ta yaya za mu yi hakan zai yiwu?

**Ali:** Da farko dai sai mu kauce wa abin da ya fi ƙarfinmu, ko?

**Jamila:** Me kake nufi?

**Ali:** Ina nufin mu yi rayuwa irin ta 'idan ba ni da gashin wance, kada na ce sai na yi kitson wance'.

**Bash:** Ban gane ba.

**Ali:** Bari na yi amfani da kai Bash, na ba da misali. Bai kamata a ce ka ciwo bashin keke ba wai don kai ma kana so a makaranta ka zama kamar irin 'yan baba-na-da-rai.

**Bash:** Wato kana nufin na tsaya a matsayina ke nan, na dinga dukan sayyadata zuwa makaranta?

**Ali:** E mana. Idan ba ka da kuɗin sayen abu, ka manta da shi kawai! Mene ne amfanin cin bashi ko rance wanda daga

ƙarshe zai jefa ka a cikin halin da muka tsinci kanmu yanzu? Ga hannun Jamila fa a karye, kuma ga shi mu sai faman noma muke a caji'ofis sai ka ce wasu masu laifi.

**Yallaɓai:** Kai! Ku ci gaba da aiki kafin na zo kanku!

**Fitowa ta 4: A caji'ofis**

**Sakatariya:** Alo? Nan ofishin 'yan sanda ne. … To ina zuwa, riƙe waya! … Kai ake nema, Yallaɓai.

**Yallaɓai:** Wane ne?

**Sakatariya:** Ya ce sunansa Audu. Ka kira shi ne ba ka same shi ba, shi ya sa ya bugo.

**Yallaɓai:** Alo Malam Audu. … E, to. ... Haka ne. Abin da ya sa na kira ka, ina so ne don Allah ka taimaka ka gabatar da '*lecture*' ga ɗaliban garin Kwazaye a kan haɗarin cin bashi. … E mana. Ai wajibi ne ka yi amfani da irin basirar da Allah Ya ba ka, ka taimaki 'yan garinku. Akwai rigingimu na cin bashi barkatai. … Haka ne. A zancen nan da muke akwai rigingimu da yawa da nake fama da su. … Ai kuwa da na ji daɗi. … Na gode, sai an jima.

**Mai ba da labari:**
A wannan yammancin baban Bash, wato Malam Lawan, ya dawo. Da ma ba ya gari saboda ya je dubiyar ɗan'uwansa, kuma an ba shi labarin abubuwan da suka faru tun kafin ya isa gida. To, kamar yadda kuke zato, a fusace ya isa gida.

**Fitowa ta 5: A gidan su Bash**

**Nana:** Haba Bakwaloji, ki tsaya mana! Ki tsaya na ƙarasa tatsar. Ina fa da aiki a gabana. Don Allah ki tsaya! Yauwa 'yar kirki! To ba ga shi ba!

**Lawan:** Na samu labarin cewa ashe ɗanki mai laifi ne ko?

**Nana:** Haba Maigida! Ni har ka tsorata ni! Sai ka ce wani a-karaɗa!

**Lawan:** Tambayarki nake!

**Nana:** Haba Maigida! Ko gaisuwa ma babu! Satinka biyu fa ba ka gari! Ka shigo mini sai ka ce ba ka taɓa ganina ba!

**Lawan:** Yana ina? Ina Bash ɗin ya shiga?

**Nana:** Yana ciki. Dawowarsa ke nan daga caji'ofis.

**Lawan:** To, ki faɗa masa maza-maza ya bar min gida!

**Nana:** Haba Maigida! Tsaya mana! Bash fa ɗanka ne. Ai bai kamata ka yi masa korar kare ba!

**Lawan:** Idan dai yana son zama a gidan nan, sai ya biya rikodar da aka ce min ya sata.

**Nana:** Haba Maigida, ai to ba shi kaɗai ba ne. Shi da Ali da Jamila ne! Ka kuma san cewa ba shi kaɗai zai biya ba ko?

**Lawan:** Amma ai saboda kekensa ne, ko ba haka ba?

**Nana:** Haba Maigida, ka tsaya mana! Kada ka yi haka mana, Maigida!

**Lawan:** Na yi! Ni na tafi gareji, zan je in ga yadda aiki ke tafiya. Ba kuma na so in dawo na same shi a nan!

**Nana:** Haba Maigida, ka saurara min mana! Maigida! Ka dawo mana! Haba!

**Mai ba da labari:**
Amma ina! Baban Bash ko ma waiwayowa bai yi ba! Nan aka bar Maman Bash riƙe da ƙwaryar tatsa! Ko ta ina Bash zai samu kuɗin nan ya biya masu bin sa bashi? Ina kuma zai tafi tun da babansa ya kore shi daga gidansa? Waɗannan su ne jawaban da zan yi muku idan muka sake saduwa. Za ku iya samun ƙarin bayani a kan shirye-shiryen nan na “Ji Ka Karu” a adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kuna kuma iya saduwa da mu a shafinmu na ‘Facebook’. Ni kuma na yi gida! Sai mun sadu, ku huta lafiya!